# Nazari da Damawa da Kowane Jinsi

*(daga Bayanan Jagoranci Game da Damawa da Kowane Jinsi na USAID)*

## Za ku iyazaɓen tambayoyi ta la'akari da dacewarsu da rikicin da sauye-sauyen VE da ya shafi muhallin gudanar da aikinku.

### + CIKAKKUN TAMBAYOYI

- Ta wace hanya ce rawar da mata da maza ke takawa da matsayinsu a cikin al'umma zai iya yin tasiri a kan aikin da za a gudanar? Wannan ya haɗa da ɓangaren siyasa, wurin aiki, da rayuwa a gida (misali rawar da ake takawa wajen yanke hukunci).
- Ta wace fuska sakamakon da ake tsammanin na aikin zai iya yin tasiri a kan mata da maza a keɓance?

### + RAWAR DA KOWANE JINSI KE TAKAWA DA KUMA NAUYIN DA YA RATAYA A KANSU

- Shin matsayi mabambanta da mata da maza ke da shi da/ko duk waɗansu sauye-sauye ga wadannan abubuwa masu sauyawa na iya taimakawa wajen buɗe kofar jan ra'ayin mutane su faɗa harkar rikici?
- Shin nauyi mabambanta da ya rataya ga wuyar maza da mata a cikin gida na ƙarawa ko rage yiwuwar su fuskanci rikici?
- Mene ne matsayin maza da mata ta fuskar janyo mutane domin su shigar harkar rikici ko kuma su sasanta rikici?
- Shin bambance-bambancen matsayi da ake samu tsakanin maza da mata a cikin al'umma yana tasiri ga shiga harkar shugabanci da suke yi da kuma shiga harkokin bunƙasa al'umma a matakin cikin gida da matakin ƙasa?
- Shin matsayin maza da mata a cikin gida na tasiri a kan yadda ake yanke hukunci?

### + AL'ADUN DA SUKA SHAFI JINSI DA ABUBUWAN DA AKE TSAMMANI DAGA KOWANE JINSI

- Shin abin da ake tsammanta daga halayen mata a maza na sauya irin rauni da suke da shi game da tsattsauran ra'ayin rikici?
- Shin abin da ake tsammani na daga halayen mata da maza da matsayinsu na samar da matsalolin da jagorori za su iya amfani da su domin jawo hankalin mutane zuwa shiga rikici?
- Shin al'adu da suka shafi "ƙarbaɓɓun" halaye na maza da mata na ƙarfafa/daƙushe iliminsu da da sahannu a cikin al'amarin kwantar da rikici/samar da zaman lafiya?
- Shin tsammantar bambance-bambance da ake yi game da ilimin maza da mata da matakan yanke hukuncinsu da halayyarsu na tasiri a kan sadarwa da bayar da bayanai a cikin al'umma?

## + SAMUN DAMAR KAIWA GA KAYAYYAKI, BAYANAI DA KARFIN IKO

- Shinya maza yara/manya da mata yara/manya suna da kwatankwacin dama iri guda na samun damarmaki da abubuwa a cikin al'umma, kamar su ilimi, ruwa, mallakin fili, adalci, damarmakin da suka shafi tattalin arziki? Ta yaya wannan ke tasiri game da raunin da maza da mata ke da shi na faɗawa rikici?
- Ta waɗanne sigogi ne mata da maza ke riƙe da ragamar iko? Waɗanne ƙalubale ne ke tattare da nau'ukan iko da suke da shi a ɓangaren daƙile rikici? Su wane ne jagorori?
- Shin jagororin haddasa rikici na amfani da taƙaddamar jinsi a matsayin hikima? Wane rawa maza da mata ke takawa (a matsayin masu cutuwa, a matsayin waɗanda ke aikata laifi, da sauransu)? Wane tasiri wannan rikici yake da shi a kan gidaje, al'umma da zamantakewa?
- Shin bambanci da ake da shi a ɓangaren samun kuɗin shiga a gida na haifar da bambance-bambance ga nau'in rauni da ake da shi na faɗawa rikici?
- Shin maza da mata na fuskantar nau'ukan ƙalubale mabambanta yayin neman tsaro a ƙauyuka?
- Shin bambancin da ke tsakanin mata da maza ta fuskar samun kayayyakin ci gaba da 'yancin mallaka na yin tasiri a kan damar da suke da ita na jure ƙalubalen rikici a rayuwarsu da al'ummarsu?

## + TA WACE FUSKA SAKAMAKON DA AKE TSAMMANIN NA AIKIN ZAI IYA YIN TASIRI A KAN MATA DA MAZA A KEƁANCE?

- Ta wace hanya ce rawar da mata da maza ke takawa da matsayinsu a cikin al'umma zai iya yin tasiri a kan aikin da aka ƙudurta gudanarwa? Wannan ya haɗa da ɓangaren siyasa, wurin aiki, da rayuwa a gida (misali rawar da ake takawa wajen yanke hukunci).
- Shin ƙarfafa halartar da maza suke yi ga aikin zai kassara ko ya ƙarfafa wa mata guiwa tare da ba su damar cin gashin kansu?
- Ta wace fuska ayyukan da suka gabata masu kama da wannan suka yi tasiri a kan bambance-bambancen jinsi a cikin gidaje da cikin al'umma?
- Game da shirye-shiryen ƙarfafa mata, shin wadataccen ilimi ga mata da kuma damar da suke da ita na samun kayayyaki zai ƙara musu haɗarin tashin hankalin cikin gida? Shin idan maza suka saka hannu za a samu sassaucin wannan haɗari?
- Shin ayyukan ƙarfafa mata zai yi tasiri a kan sauye-sauyen ƙarfin ikon gida da samar da kayayyaki? Shin ana iya samun wata matsalar da ba a shirya mata ba? Ta yaya za a ku iya shawo kansu?
- Shin gabatar da ayyukan zamanlafiya da sasantawa na magance tazarar da ke tsakanin al'adun da suka shafi jinsi da kuma rashin daidaito?

Da zarar kun zaɓi tambayoyinku, to ku yi amfani da takardar aikin da ke ƙasa domin amsa su.

| | |
|---|---|
| CIKAKKUN TAMBAYOYI | |
| RAWAR DA KOWANE JINSI KE TAKAWA DA KUMA NAUYIN DA YA RATAYA A KANSU | |
| AL'ADUN DA SUKA SHAFI JINSI DA KUMA ABUBUWAN DA AKE TSAMMANI DAGA KOWANE JINSI | |
| SAMUN DAMAR KAIWA GA KAYAYYAKI, BAYANAI DA KARFIN IKO | |
| TA WACE FUSKA SAKAMAKON DA AKE TSAMMANIN NA AIKIN ZAI IYA YIN TASIRI A KAN MATA DA MAZA A KEƁANCE? | |